# Baftisma da Kuma Dangantakarka da Allah

(Sashe na 2)

An ɗauko daga babi na 18 na littafin nan *Menene Ainihi Littafi Mai Tsarki Yake Koyarwa?* za a iya samunsa a dandalin jw.org/ha.

**MANUFA: Ka bincika abin da ka yi imani da shi da kuma dalilin da ya sa ka yi hakan, kuma ka bincika abin da Littafi Mai Tsarki ya koyar don ka iya bayyana ma wasu abin da ka yi imani da shi.**



## MENE NE MUTUM ZAI YI KAFIN A YI MASA BAFTISMA?

### 1 KA BINCIKA ABIN DA KA YI IMANI DA SHI

Me kake ganin wasu mutane za su ce?

________________________________________

________________________________________

Me *ka* yi imani da shi?

________________________________________

________________________________________

Me ya sa ka yi imani da hakan?

________________________________________

________________________________________



www.jw.org/ha © 2017 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

## 2 KA BINCIKA ABIN DA LITTAFI MAI TSARKI YAKE KOYARWA

**Kafin a yi wa mutum baftisma, wajibi ne ya yi rayuwar da ta jitu da nufin Allah.**
(Ka duba babi na 18, sakin layi na 8-13 na littafin nan *Menene Ainihi Littafi Mai Tsarki Yake Koyarwa?*)

**Karanta Irmiya 20:9; 2 Korintiyawa 4:13.**
Me ya kamata bangaskiyar Kirista ta motsa shi ya yi?

________________________________________

________________________________________

________________________________________

**Karanta Ayyukan Manzanni 3:19.**
Kafin mutum ya yi alkawarin bauta wa Allah, waɗanne matakai ne ya kamata ya ɗauka?

________________________________________

________________________________________

________________________________________



**Idan ka ba abokinka kyautar mota, ba za ka riƙe maƙullin motar ko kuma ka nace cewa kai ne za ka riƙa tuka motar ba. Hakazalika, idan ka yi alkawarin bauta wa Jehobah, wajibi ne ka yi dukan abin da ya ce ka yi**


www.jw.org/ha © 2017 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

## Wajibi ne mutum ya yi alkawarin bauta wa Allah kafin a yi masa baftisma.

(Ka duba babi na 18, sakin layi na 14-16 na littafin nan *Menene Ainihi Littafi Mai Tsarki Yake Koyarwa?*)

**Karanta Kubawar Shari’a 6:15; Markus 8:34.**

Mene ne yin alkawarin bauta wa Allah yake nufi?

**Karanta 1 Bitrus 4:2.**

Ta yaya ɗaukan alkawarin bauta wa Allah yake iya shafan rayuwar mutum da kuma makasudansa?

Waɗanne canje-canje ne ka yi don ka yi rayuwar da ta jitu da nufin Allah, kuma waɗanne canje-canje ne kake so ka yi a nan gaba?



www.jw.org/ha © 2017 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

## 3 KA BAYYANA ABIN DA KA YI IMANI DA SHI

IDAN WANI YA CE…

**Ba dole ba ne Kiristoci su yi wa'azi. Allah yana so mu zama mutanen kirki ne kawai.**

ZA KA IYA CE…

**Ba mamaki, wasu mutane sun yarda da wannan ra'ayin. Amma a ganina hakkina ne in yi wa mutane wa'azi domin…**

_______________

_______________

Wane nassi ne za ka iya karanta wa mutumin?

_______________

Bisa ga ra'ayin mutumin, ta yaya za ka bayyana wannan nassin?

_______________

IDAN WANI YA CE…

**Masu tsattsauran ra'ayi ne kawai za su iya bauta wa Allah da dukan zuciyarsu.**

ZA KA IYA CE…

**Na san cewa Allah ba ya so mu kasance masu tsattsauran ra'ayi. Amma na yi imani cewa ya kamata mu bauta wa Allah da zuciya daya domin…**

_______________

_______________

Wane nassi ne za ka iya karanta wa mutumin?

_______________

Bisa ga ra'ayin mutumin, ta yaya za ka bayyana wannan nassin?

_______________


www.jw.org/ha © 2017 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania